# IDAN KA MUTU YAU INA ZA KA?

**Alhali kuwa ba ku san abin da gobe za ta kawo ba. Wane iri ne ranku? Ai, kamar hazo yake, jim kaɗan sai ya ɓace. YAKUBU 4:14**

**AKWAI GASKIYA GUDA HUƊU WAƊANDA MUKE BUƘATAR FAHIMTA:**

## 1 YESU YANA SON KU.

**YANA SO KU SAMI RAI MADAWWAMI TARE DA SHI A SAMA.**
**Domin Allah yana ƙaunar duniya har ya ba da makaɗaicin Sonansa, domin duk wanda ya gaskata da shi kada ya lalace, amma ya sami rai madawwami. YAHAYA 3:16**

**YANA SON KU SAMI CIKAKKIYAR RAYUWA MAI MA'ANA TARE DA SHI.**
**Barayi suna zuwa ne kawai don yin sata, kisa, da lalatawa. Na zo ne domin su sami rai, su kuma cika shi sarai. YAHAYA 10:10**

**KOYAYA, MUTANE DA YAWA BA SA RAYUWA MAI MA'ANA KUMA BA SU DA TABBACIN KO SUNA DA RAI MADAWWAMI SABODA ...**

## 2 MUTUM BISA GA DABI'ARSA ZUNUBI NE. SHI YA SA YA RABU DA ALLAH.

**DUKAN MUTANE MASU ZUNUBI NE.**
**Gama 'yan adam duka sun yi zunubi, sun kasa kuma ga ɗaukakar Allah. ROMAWA 3:23**
**HUKUNCIN ZUNUBI MUTUWA NE.**
**Gama sakamakon zunubi mutuwa ne...ROMAWA 6:23**

**AKWAI NAU'I BIYU NA MUTUWA DA AKA AMBATA A CIKIN LITTAFI MAI -TSARKI:**
- **MUTUWAR JIKI**

**Tun da an ƙaddara mutum ya mutu sau ɗaya kawai, to akwai hukunci. IBRANIYAWA 9:27**

- **MUTUWA TA RUHANIYA KO RABUWA TA HAR ABADA DAGA ALLAH**

**Amma matsorata, da marasa riƙon amana, da masu aikin ƙyama, da masu kisankai, da fasikai, da masu sihiri, da masu bautar gumaka, da kuma duk maƙaryata, duk rabonsu tafkin nan ne mai cin wuta da kibiritu, wanda yake shi ne mutuwa ta biyu. WAHAYIN 21:8**

**IDAN MUTUM YA RABU DA ALLAH SABODA ZUNUBINSA, MENENE MAGANIN WANNAN MATSALAR?**

**SAU DA YAWA MUNA TUNANIN CEWA WAƊANNAN SUNE MAFITA: ADDINI DA AYYUKAN ALHERI DUK DA HAKA, AKWAI MAFITA GUDA ƊAYA DA ALLAH KE BAYARWA.**

## 3 YESU KRISTI SHINE KADAI HANYAR ZUWA SAMA.

**Yesu ya ce masa, Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai: ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina. YAHAYA 14:6**

**YESU YA BIYA DUKAN ZUNUBAN MU.**
**Domin Almasihu ma ya mutu sau ɗaya tak ba ƙari, domin kawar da zunubanmu, mai adalci saboda marasa adalci, domin ya kai mu ga Allah...1 BITRUS 3:18**

**YESU YANA DA ALKAWARIN RAI MADAWWAMI.**
**Wanda ya gaskata da Ɗan, yana da rai madawwami. Wanda ya ƙi bin Ɗan kuwa, ba zai sami rai ba, sai dai fushin Allah ya tabbata a gare shi. YAHAYA 3:36**

## 4 MUNA BUƘATAR SANYA BANGASKIYARMU CIKIN UBANGIJI YESU KRISTI DON SAMUN CETO.

**ALHERIN ALLAH YANA KAWO CETO TA WURIN BANGASKIYA CIKIN YESU KIRISTI.**
**Domin ta wurin alheri ne aka cece ku saboda bangaskiya, wannan kuwa ba ƙoƙarin kanku ba ne, baiwa ce ta Allah, ba kuwa saboda da aikin lada ba, kada wani ya yi fariya. AFISAWA 2:8-9**

**YI WANNAN ADDU'AR TARE DA IMANI:**
**UBANGIJI YESU, NA GODE DA KAUNARKA A GARE NI. NA FURTA CEWA NI MAI ZUNUBI NE KUMA INA NEMAN GAFARAR KU. NA GODE DA KUKA MUTU AKAN GICCIYE DON BIYAN BASHIN ZUNUBAINA. DAGA YANZU, NA DOGARA GARE KU A MATSAYIN UBANGIJINA DA MAI CETONA. NA KARƁI KYAUTAR KU TA RAI MADAWWAMI KUMA NA BA KU RAINA. KA TAIMAKE NI IN YI BIYAYYA DA UMARNANKA, DON IN FARANTA MAKA RAI. AMIN.**

**IDAN KUN YI IMANI DA YESU KRISTI, WAƊANNAN ABUBUWA SUN FARU DA KU:**
- **YANZU KUNA DA RAI MADAWWAMI. YAHAYA 6:40**
- **DUK GAFARAR ZUNUBANKU. (BAYA, YANZU, NAN GABA) KOLOSIYAWA 1:13–14**
- **YANZU KUN ZAMA SABUWAR HALITTA. SHINE FARKON SABUWAR RAYUWAR KU. 2 KORANTIYAWA 5:17**
- **YANZU KAI DAN ALLAH NE.**
  **Amma duk waɗanda suka karɓe shi, ya ba su ikon zama 'ya'yan Allah, har ma ga waɗanda suka ba da gaskiya ga sunansa. YAHAYA 1:12**